Idan ɗayanku ya ji wani abu a cikinsa, sai ya rikitar da shi cewa shin wani abu ya fita daga gare shi ko a'a, to, kada ya fita daga masallaci har sai ya ji kara ko ya ji waji wari

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Idan ɗayanku ya ji wani abu a cikinsa, sai ya rikitar da shi cewa shin wani abu ya fita daga gare shi ko a'a, to, kada ya fita daga masallaci har sai ya ji kara ko ya ji waji wari".

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi -yana bayyana cewa idan wani abu ya yi kai-kawo a cikin cikin mai sallah, sai ya rikitar da shi; shin wani abu ya fita daga gareshi ko a'a? to, kada ya fita daga sallarsa ya yanketa don sake alwala, har sai ya tabbatar da samun karin da ya ɓata alwalarsa; ta hanyar ya ji karar tusa, ko ya ji wari; domin abin aka tabbatarw to kokwanto ba ya ɓata shi, shi tabbas ya tabbatar da tsarki (alwala) kari kuma akwai kokwantone a cikinsa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/65083